Lallai Ibrahim Xana ne, kuma ya Mutu a na shayar da shi, kuma lallai yana da Masu shayarwa guda biyu da zasu qarasa masa shayarwa a cikin Al-janna.

An rawaito daga Anas Bn Malik -Allah ya yarda da shi- ya ce: "ban tava ganin wanda yake mafi jin qan Manzon Allah ba SAW ga Iyalansa ya ce: "Ibrahim ya Kasance ana shayar da shi a Awalin Madina, sai manzon Allah ya tafi muna tare da shi, sai ya shiga gida sai ya shiga gidan kuma shi ana yi masa hayaqi, kuma mai shayar da shi Baiwa ce sai ya karve shi sai ya sumbance shi, sannan ya dawo" Amr ya ce:yayin da Ibrahim ya rasu sai Manzon Allah SAW ya ce: "Lallai Ibrahim Xana ne, kuma ya Mutu a na shayar da shi, kuma lallai yana da Masu shayarwa guda biyu da zasu qarasa masa shayarwa a cikin Al-janna"

[Ingantacce ne] [Muslim ne ya rawaito shi]

Anas -Allah ya yarda da shi- yana bada labari cewa shi ba tava ganin wanda yake mafi jin qan Manzon Allah ba SAW ga Iyalansa ya ce: "Ibrahim ya Kasance ana shayar da shi a Awalin Madina, sai manzon Allah ya tafi muna tare da shi, sai ya shiga gida sai ya shiga gidan kuma shi ana yi masa hayaqi, kuma mai shayar da shi Baiwa ce sai ya karve shi sai ya sumbance shi, sannan ya dawo" Amr ya ce:yayin da Ibrahim ya rasu sai Manzon Allah SAW ya ce: "Lallai Ibrahim Xana ne, kuma ya Mutu a na shayar da shi, kuma lallai yana da Masu shayarwa guda biyu da zasu qarasa masa shayarwa a cikin Al-janna kuma ya rasu ne yana Xan shekara Shida ko wata goma sha bakwai sai wasu masu shayarwa biyu suka ci gaba da shayar da shi ya cika shekara biyun saboda shi ne cikar Shayarwa da nassin Qur'ani, Kuma wannan Karama ce gare shi da Mahaifinsa SAW.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/11188